**Habibullah Abuu Abdirrahman**

April 13 ·

SHAHADAR KHADIMUL QUR'AN

Yau shekaru 12 cif da 'yan Boko Haram suka zubar da jini mafi tsada a Nigeria jinin Sheikh Ja'afar Mahmud Adam Kano, wanda muke kyautata masa zaton ya dace da mutuwar shahada insha Allah

Shahararren kwamandan kungiyar Boko Haram Ibrahim Al-muhajir Uqubah wanda yafi shahara da sunan Alhaji Fari shine ya jagoranci kisan gillar da suka yiwa Malam Ja'afar


Sai dai wani labari mai dadi jama'a; Alhaji Fari ya jagoranci kisan Malam Ja'afar da bindiga kirar AK47 sukayi ajalinsa, shi kuma Alhaji Fari tankar yakin sojojin Nigeria ita tayi ajalinsa, takashi tayi ta markade tsinanne a garin Bama jihar Borno a shekarar 2014 ranar da ya jagoranci 'yan uwansa 'yan ta'adda sukayi hari suka fasa dakin ajiyar makaman sojoji na karkashin kasa

Tsakanin wanda harsashin bindiga kirar AK47 tayi ajalinsa da wanda tankar yakin sojoji tayi ajalinsa ta takashi aka markade buzun gawansa a kasa wannene yafi yin mutuwar wulakanci jama'a?

Karshen rayuwar kenan, Alhaji Fari ya tafi gurin da Malam Ja'afar yaje, sai ranar Hisabi Malam Ja'afar zai tashi jinin jikinsa yana zuba yana fitar da kamshin turaren Almiski, ya shako wuyan Alhaji Fari zuwa gaban Allah yace Allah gashi nan ka tambayeshi laifin me nayi ya zubar da jini na?

Allah Ka kyautata makwancin Malam Ja'afar da na aboki amininshi Malam Albaniy Zaria
Allah Ka karbi shahadarsu Ka hada fuskokinmu da nasu a cikin Aljannah Madaukakiya Amin

See Translation






46

23 Comments 13 Shares